For
**What is Breast Cancer**
in other languages, like French, Yoruba, Igbo and English
visit
**www.socron.net**

**Tsari da Wallafawa na**
Farfesa Clemant A. Adebamawo.
Ɓangaren cututtukan Kansa
Sashen Fida, Asibitin Koyarwa na Ibadan Jihar Oyo Nigeria.
i-mel: clementadebamawo@yahoo.com

Mai fassara: Aisha Umar, MSc Hausa, BUK



# Memene sanƙaran mamaƙ



Hausa

# Memene sanƙaran mamaƙ

Sanƙaran mama na afkuwa ne a yayin da ƙwayoyin halittar jikin mama suka fara girma a kan kansu ba tare da jiki ya umarce su ko ya buƙace su da su yi haka ba.
Wannan hoto na sama ya nuna mama da cutar sanƙara ta fara kama shi. Wanda za a iya warkar da shi, domin bata dade da kama shi ba. Idan aka duba jikin wannan hoto za a ga cewa babu wani canji a jikin maman. Kuma matar da take dauke da wannan cutar ba ta cikin rashin lafiya, kawai dai akwai dan wani dan tsiro karami (wanda yake jeji ne) a cikin mamanta.

### Me yake jawo sanƙaran mamaƙ

Mutane da dama sukan so su san abinda yake jawo wannan cuta ta sanƙaran mama. Har ma sukan tambayi kansu, me yasa na gamu da wannan cutaƙ Ko me ya sa matata ko ƙanwata ko ya ta ko ƙawata ta gamu da wannan cutaƙ Ko akwai wani abu da na yi ko suka yi, da ya kamata su yi, ko na yi, da banyi ba, ko basu yi ba domin kare kai na ko kansu daga wannan cutaƙ.

Babu wani sanannen dalili da za a iya kawowa kai tsaye wanda za a ce shi yake kawo wannan cuta. Sai dai akwai wasu dalilai da sukan sanya wannan cuta ta fi saurin kama wasu matan a maimakon wasu.
Waƙannan dalilai su ne:

- **Shekaru** – ƙarfin zaton kamuwar mace da sankaran mama, yana karuwa ne da yawan shekarun mace.
- **Sinadarin iyistirogin** – Yawan Sinadarin iyistirogin da yake jikin mace. Shi wannan sinadari na iyistirogin yana ƙaya daga cikin sinadaran da jikin mace ya ƙunsa kuma yana da kyau a ce jikin mace yana da wannan sinadari isashshe. Sai dai kuma bai kamata a ce jiki yana fitar da shi ba tare da hutu ba. Wannan hutun yana zuwa ne a lokacin da mace take da ciki ko take shayarwa. Don haka dalilan da suke haifar da kasancewar sinadarin iyistirojin a jiki suna jefa jiki cikin haƙarin kamuwa da cutar sanƙaran mama. Daga ciki akwai fara jinin al'ada da wuri (kafin a kai shekara goma sha biyu), yin al'ada har a wuce shekara hamsin da biyar, rashin haihuwa, da kuma jinkirin haihuwa da wuri har a wuce shekara talatin. Waƙannan abubuwa ba yin kanmu ba ne, kuma za a iya saisaita yawan wannan sinadari a jiki ta hanyar shan magungunan hana ƙaukar ciki da na sa haihuwa da sauransu.
- **Girman Jiki da sura -** Mace mai tsaho da mace mai ƙiba ta fi faƙawa hadarin kamuwa da wannan cuta. Matan da sukayi ƙiba kuma basu rame ba har bayan sun daina jinin al'ada haƙarin kamuwarsu da sanƙaran mama yafi yawa. Haka kuma komai shekarun mace, wanda suke da tarin kitse a tumbin su ko kuma a ƙugun su suma hadarin kamuwarsu da sankaran mama yafi yawa
- **Tarihin cuta a cikin 'yan uwa** – Macen da a cikin yan uwanta an taƙa samun wata kamar mahaifiyarta, ko yarta, ko 'yarta ta tana da wannan cuta, ta fi fadawa haƙarin kamuwa da wannan cuta.
- **Tarihin Kamuwa da cutar Sanƙaran mama:** Macen da cutar sanƙara ta taƙa kama ta a mamanta guda ƙaya, cutar za ta iya kama ƙaya maman ma sanƙara daga baya
- **Wasu cututtukan mama da ba sanƙara ba:** Wasu matan da aka taƙa cire musu tsiro a mamansu wanda likita ya ce musu ba sanƙara bane. Dole sai suna zuwa a na duba wannan mama akai-akai domin irin wannan tsiro zai iya juyawa ya koma cutar



Akwai tabbacin cewa kamuwa da cutar sanƙaran mama ba laifin mutum ba ne. Bata da alaƙa wacce take kai tsaye da abincin da muke ci, kuma ba cuta bace mai kwayoyi da za'a iya kamuwa dasu ba. Haka kuma ba a daukar ta ta hanyar jima'i, ko ta hanyar hulda da wanda yake da wannan cuta.

**Ta ya ya mutum zai ake gane sanƙaran mamaƙ**
Abu na farko da za a fara lura a tabbatar da cewa jiki ya kamu da cutar
sanƙaran mama shine samuwar wani dan tsiro a cikin nonon maras ciwo. Shi wannan tsiro za a ji shi kamar kurjin maruru sai dai ba ya ciwo. Duk macen da ta ji irin wannan a jikin mamanta sai ta garzaya wajen likitanta nan take. Dole ne a cire duk ilahirin irin wannan tsiron sannan a gwada a asibiti. Maman da cutar sanƙara ta fara kamashi in an kalle shi a ido ba za a ga wani canji ba, haka kuma a jiki ma ba za a ji komai ba. **Ba ya kawo ciwo, baya sa zazzabi, amai, gudawa ko rashin cin abinci kuma ba ya hana ayyukan yau da kullum. Ba lallai ba ne a ce kin taƙa ganin ko jin labarin cutar ba, domin mai yiwuwa ne a ce bata taƙa kama wani dan uwanki ba ko wanda kika sani. A wannan mataki na farkon shigar wannan cutar akwai fatan cewa in dai aka yi maganin wannan cutar za a iya warkar da ita.**



Sanƙaran mama kuma tana iya farawa ta hanyar fitowar ciwo a kan mama ko fatar da ta zagaye kan maman.



A wasu matan kuma, kan nonon ne zai fara shigewa ciki. Za'a ga mazaunin sa ba daya yake dana ƙaya ƙangaran ba.
Idan aka kalli wannan hoton da yake ƙasa da hoton farko a wannan takardar za'a ga cewa akwai fitacccen kumbiri a saman kan maman, kuma shi kansa kan maman girmansa da mazauninsa ya canza.



A nan cutar ta riga ta haƙaka don haka ya kamata a ce an zo asibiti tun kafin cutar ta kawo wannan matakin. Idan aka kyale tsiron, ci gaba zai yi tayi da girma. Zai iya girma daga cikin maman har ya ratso fatar maman ya zamo gyambo (ciwo) wanda yake fitar da ruwa da jinni mai wari, kuma ba zai warke ba sai anyi maganin wannan cuta.

A sa'ar da wannan cuta ta cigaba da bunƙasa, ta kan bazu zuwa wasu sassa na jiki kamar ƙwaƙwalwa, hunhu, kasussuwa da hanta ta wata hanya da ake kira (Metastasis) da turanci. Ita wannan bazuwar zuwa ga wadannan gabobin ne ke cutarwa, kuma da zarar hakan ta faru, duk da cewa bayar da magani ya zama dole, samun waraka abu ne mai wahala.

Za a iya gane irin wannan buzuwar cutar ta hanyar samuwar tari, haki, kumburin ciki, ciwo a kasussuwa musamman ma baya, rashin ƙarfin ƙafafu da rashin iya motsa su.

**Shin za a iya gane cutar sanƙaran mama da wuriƙ**
Za'a iya gane wannan cuta da wuri ta hanyar lura da halin da maman ke ciki. Wannan wadansu matakai ne da mace zata riƙa bi sau daya a wata domin ta duba mamanta ko akwai wani tsiro, kumburi, ko wata cuta a jikin maman. Ya kamata ki buƙaci likitanki tkoya miki yadda zaki riƙa duba mamanki ita ma kuma ta duba miki mamanki a ƙalla sau daya a shekara. Daukan hoton mamman a asibiti don binciken cutar, na iya taimakwa wajen gano tad a wuri.

**Matakan Sanƙaran Mama**
Ana iya fahimtar tsanin bazuwar da wannan cuta tayi a jikin marar lafiya ta hanyar matakin da cutar take a wannan lokacin. Waƙannan matakai su ne:

**Mataki na I:** Tsiron cikin maman da bai kai sentimita biyu ba, ko kuma yana daidai da sentimita biyu. Kuma idan aka gwada kaluluwar hammata za'a ga babu wannan cuta.

**Mataki na II:** Faƙin tsiron cikin maman yana tsakanin sentimeta biyu zuwa biyar tare da kaluluwar hammata wacce ta nuna akawai cuta ko kuma wacce ta nuna babu cutar. Zai kuma iya kasancewa faƙin tsiron cikin maman ya wuce sentimeta biyar tare da kaluluwar hammata wacce ta nuna cewa akwai cutar.

Mataki na III: Wannan matakin an kasa shi zuwa gida biyu IIIA da IIIB.

**IIIA:** A nan faƙin tsiron cikin maman ya fi sentimita biyar, kuma akwai kaluluwar hammata masu motsi waƙanda suke dauke da wannan cuta. Ko kuma girman kumburin zai iya zama ko ma ya ya da kuma kaluluwar wacce kaluluwar hammata waƙanda suka maƙalewa juna kokuma suna maƙale da wata tsoka dake wannan gurbin.

**IIIB:** A nan faƙin tsiron cikin maman zai zama ko yaya amma ya bazu zuwa fata, bangon ƙirji, ko kaluluwa da suke can kasan nono kuma a can cikin ƙirji.
Mataki IV: A nan faƙin tsiron cikin maman ko ma ya girmansa yake anan ya bazu zuwa wurare masu nisa kamar ƙasussuwa, hunhu, ko kaluluwar jiki da suke nesa da mama.

Mataki na I da na II su ne farkon kamuwa da wannan cuta amma mataki na III da IV cutar ta riga ta bunƙasa.

Yaya ake maganin cutar sanƙaran mamaƙ
Ana maganin sanƙaran mama sabuwar kamu ta **wadannan hanyoyi:**
Surgery (Fiƙa): Wannan shine a cire maman gaba daya ko wani ƙangarensa ta hanyar fida. Amma yin wannan fiƙa ya danganta da abubuwa da dama wanda zaki tattauna da likitanki.

**Chemotherapy -** Shine yin amfani da magani domin a kashe ƙwayoyin da suka gina wannan cuta, wadda ta riga ta bazu zuwa wasu ƙangarori na jiki ko a ƙanƙantar da wannan kumburi na mama. Duk da dai waƙannan magunguna su na da illoli, amma akwai hanyoyin da likitoci sukan bi domin taimakawa mai wannan cuta wajen samun saukin waƙannan illoli.

**Hormone Treatment -** yin amfani da wannan sinadari na homon domin su hana ƙwayoyin wannan cuta girma. Za a iya yin wannan ta hanyar fiƙa, radiotherapy, ko shan da magunguna.

**Radiotherapy -** yin amfani da ƙwayoyi na wuta wajen kashe ƙwayoyin wannan cuta.

Akwai hanyoyi da dama da ake bi a warkar da wannan cuta, sai dai ya danganta da bazuwarta a jiki, zabin mai ƙauke da wannan cuta, kuƙin da za'a iya kashewa, da yadda za a iya daurewa bin ƙa'idojion shan magani, da kuma kayan aiki da ake da su.
Yin maganin wannan cuta ya kan ƙau lokaci mai tsaho kuma ana buƙatar yawan zuwa asibiti. Yana da tsada kuma yakan dau lokaci. Duk wadannan abubuwa ne da suka zama dole a tattauna su da likita.
Haka kuma yana da kyau mai ƙauke da cutar sanƙaran mama ta tattauna da 'yan uwanta domin su gane yadda cutar take domin su ba ta goyon baya da ƙwarin gwiwa, kuma su taimaka wajen faƙakarwa game da lura da mama.

**Sakamakon magani**

Karbar magani ga jiki ya bambanta daga mutum zuwa mutum kuma ya danganta da:-



- ƙ Matakin cutar a lokacin da aka gano ta: Cutar da aka gano ta tunda wuri tafi saukin warkarwa.
- ƙ Yanayin cutar sanƙara: Sauƙin warkewar ya danganta da irin cutar sanƙarar da ta kama mutum. Ana gane irin cutar ne bayan an yi gwaje-gwaje akan tsiron da aka ciro daga jikin mai ƙauke da cutar.
- ƙ Bin ƙa'idojin magani ba tare da kuskerawa ba.

Idan babu kumburi a hammata kuma girman sanƙaran bai wuce girman sentimita uku ba ko ƙasa da haka, kashi casa'in da tara cikin dari na waƙannan majinyatan sukan rayu har tsahon shekara biyar. Haka kuma kashi sittin cikin dari na majinyatan da suke da kaluluwar hammata guda biyu zuwa hudu za su iya rabuwa da cutar a cikin shekara biyar in aka haƙa da kashi arba'in cikin dari na masu ƙauke da kaluluwa shida zuwa goma.

Idan kuma cutar ta riga ta bunƙasa faƙ A na nufin kenan ba za ta warke baƙ To in da rai da robo. Domin ƙididdigar da aka bayar a sama, ta samu ne ta hanyar hada sakamakon mutane da yawa da aka yi. Babu likitan da zai ce lallai yadda aka samu din nan, haka ne zai faru a kanki, koda a ce an yi ta maganin amma cutar ta ki warkewa, likita zai iya bakin ƙoƙarinsa wajen bada magunguna waƙanda za su rage zafin cutar.

To magungunan gargajiya faƙ Abun sani anan shine, duk wanda yake jinyar mai ƙauke da cutar sanƙara, fatansa ne a samu sauƙi da wuri saboda mai cutar ta daina shan wahala. Abin takaici shine, cigaban da aka samu akan shawo kan cutar a kimiyyance bai taka kara ya karya ba. Amma duk da haka, yafi amfani nesa ba



kusa ba, yafi rashin cutarwa, kuma yafi tabbaci fiye da kowane irin hanyar magani da wani ko wata zai zo miki dashi a yanzu. A ƙarshe, mutum zai iya taimakawaa ckin binciken samo maginin da yafu na yanzu aiki ta hanyar ba da gudunmawa da haƙin kai ga masu bincike a asibiti.

Yana da mutuƙar amfani mutum ya zo asibiti da wuri da zarar ya lura da waƙansu canje-canje don neman magani.